# MUHIMMAN ƘA'IDOJI SHIDA DA SUKA SHAFI CIN ZARAFI DA CUTARWA TA HANYAR JIMA'I

1. Fahimci cewa amfani da dama dan cutarwa da cin zarafi ta hanyar jima'i daga ma'aikata **mummunar rashin ɗa'a ne kuma ya saɓa da doka** sannan kuma yana bada damar kora daga aiki.

2. **Yin ayyukan jima'i da yara (wato waɗanda ke ƙasa da shekara 18) haramun ne,** ba tare da duban yawan shekaru a garin ko dokarsu game da shekarun balaga ba. Kuskure ko rashin sani dangane da shekarun yaro/yarinya ba zai zama hujja na kariya ba.

3. **An haramta musayar kuɗi, aiki, kayayyaki ko aikace-aikace don jima'i,** har ma da wata kyautatawa don jima'i, ko sauran wasu irin nau'ikan wulaƙanci, Kunyatarwa, ko kuma halin zalunci. Da ya haɗa da musayar taimako zuwa masu karɓar tallafi.

4. **Duk wata mu'amalar jima'i** tsakanin masu bayar da taimako da kariya da kuma mutumin da ke karɓar wannan taimako da kariyar da ta ƙunshi amfani da shi ta hanyar da bai dace ba haramtacce ne. Irin waɗannan dangantaka na ɓata nagarta da mutuntakar masu aikin agaji.

5. Idan ma'aikacin agaji yana da wata damuwa ko tuhuma dangane da cin zarafin jima'i ko cutarwa ta hanyar jima'i daga wani ma'aikaci, ko da a cikin ƙungiya daya suke ko daban, **dole ne shi ko ita dole ne su kai rahoton** wannan damuwar ta hanyoyin kai rahoto da aka samar.

   Tuntuɓi: Sashin tuntuba na PSEA ko Shugaban ƙungiya
   Kira kai tsaye: 0800-000-2022
   E-mail: nga.psea@humanitarianresponse.info

6. Dole ne ma'aikatan agaji **su samar da ingantaccen** muhallin bada kariya daga cin zarafi da cutarwa ta hanyar jima'i kuma dole ne su **inganta aiwatar da ka'ɗojin aiki.** Manajoji a kowane matakai suna da nauyi a kansu don tallafawa da haɗa kan tsarin da ke kula da wannan yanayin.